


# RAYUWA DA ƘARFAFA ILIMI DA MAKARANTUNSA DA WASU HIDIMOMIN RAYUWA A ZUKATAN ZAMFARAWA, A JIHAR ZAMFARA


**Daga**

**SA'IDU MUHAMMAD GUSAU**

**SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA, JAMI'AR BAYERO, KANO, TSOHON MALAMI A ATC, MARU, BABBAR KWALEJIN KOYARWA TA MARU, JIHAR ZAMFARA**

# RAYUWA DA ƘARFAFA ILIMI DA MAKARANTUNSA DA WASU HIDIMOMIN RAYUWA A ZUKATAN ZAMFARAWA A JIHAR ZAMFARA

**SA'IDU MUHAMMAD GUSAU**

**SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA, JAMI'AR BAYERO, KANO,**
**TSOHON MALAMI A ATC, MARU, BABBAR KWALEJIN**
**KOYARWA TA MARU, JIHAR ZAMFARA**

**TAKARDAR DA AKA GABATAR DON TUNAWA DA**
**YIN ADDU'A GA FARFESA M.A.Z. SANI, SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA, JAMI'AR BAYERO, KANO**

**ALHAMIS, 30 GA SATUMBA, 2021**

**RAYUWA DA ƘARFAFA ILIMI DA MAKARANTUNSA
DA WASU HIDIMOMIN RAYUWA A ZUKATAN ZAMFARAWA
A JIHAR ZAMFAR**

**DAGA**

**FARFESA SA'IDU MUHAMMAD GUSAU, JAMI'AR BAYERO, KANO**

## 1.0 Gabatarwa

Zamfarawa mutane ne waɗanda suka shahara da mazauni a ƙasar Hausa kuma suka samar da Daular Zamfara wadda ta wanzu tun kafin ƙarni na goma sha huɗu (14). Ƙasar Zamfara ta zauna a ƙarƙashin jihadin Shehu Usmanu Ɗanfodiyo (1804-1903), sannan ta kuma zauna a farfajiyar yankin Arewa. Haka kuma ƙasar Zamfara ta taɓa zaunawa a ƙarƙashin Jihar Arewa masu Yamma ta Sakkwato tun daga 1967, kuma tun 1976 wasu gundumomi na yankin Zamfara suka zama ƙananan hukumomi. Kuma Zamfara ta koma a sabuwar Jihar Sakkwato a shekarar 1991, sannan a 1996, ranar Alhamis 1/10/1996 ta zama Jiha mai cin gashin kanta.

Daular Zamfara, Daula ce wadda ta wanzu a ɓangaren Nijeriya ta Arewa wadda kuma ta Mallaki faɗin ƙasa wanda ya kama daga Kogin Rima a sashen Arewa zuwa Gulbin Zamfara a Jihar Kudu. Ta fuskar Gabas kuwa Daular Zamfara ta yi iyaka da Dajin Rugu zuwa Dutsin Disau a Yamma (Gusau, B.M & Gusau, S.M. 2012: 20-20).



Wani Sashe na Mutanen Jihar Zamfara

Farfajiyar Daular Zamfara tana a sashen Yamma na ƙasar Hausa kuma ta sami matsayi abin girmamawa ta fuskar jaruntа kamar sauran dauloli na Katsina da Kano da Daura da Kabi da wasunsu suka samu. Haka kuma tun a ƙarni na sha huɗu (Q14) Ƙasar Zamfara ta sami manyan garuruwa waɗanda suka ƙunshi Dutsi da Birnin Zamfara da Kiyawa da Jata da Banga da Tumfafi da Alƙalawa da makamantansu. Haka kuma a ƙasar Zamfara akwai tungage da ƙauyuka da unguwanni waɗanda suka yi babban tasiri, musamman a matsayinta na Daula.

Zamfarawa mutane ne masu ƙarfi kuma ƙarfafa, masu yaji, jarumai ne kuma zarata, musamman a fagen yaƙi da kuma noma. Suna da manyan dakaru, kuma sukan iya tunkarar kowace irin runduma ta mayaƙa ba tare da sun nuna wata fargaba ko razani ba. Su Zamfarawa mayaƙa ne shahararru waɗanda suka sha kai hari na gaba a ƙasashen Zabarmawa da na Katsina da na Kano da na Yawuri da kuma na Kabi har zuwa ƙasar Adar a Jamhuriyar Nijar (Augi, 1984: 113-115).




Wata Gonar Gyaɗa da aka Shahara da Noma ta a Jihar Zamfara

Daular Zamfara kamar sauran daulolin Biladi al-Sudan, ta sami shigowar baƙin al'ummu a cikinsu daga ƙaurace-ƙauracen al'ummu a wasu sassan duniya. Gobirawa suna daga cikin baƙin al'ummu da suka fara shiga Daular Zamfara tun a zamanin Sarkin Zamfara Babba (1734) daga ƙasar Azbin a Jamhuriyar Nijar. Gobirawa sun ci gaba da isowa Zamfara rukunirukuni har zuwa lokacin Sarkin Zamfara Yakubu ɗan Faskare (1734-1739). Yawanci kuma Gobirawan sun fi zaunawa ne a garin Alƙalawa gari wanda Alƙalin Zamfara yake jagoranta.




Wasu Mutanen Daular Zamfara

Bayan da Gobirawa suka yalwata a Zamfara, sai suka haɗa kawunansu suka fuskaci Daular Zamfara, sannu a hankali cikin wayo da dabaru na kai wa Zamfara hari har sai da Gobirawa suka harɗi Daular ta Zamfara. Daular Zamfara ta faɗa hannun Gobirawa bayan mutuwar Sarkin Zamfara Maroƙi ɗan Malo a sanadiyyar sargafe kansa da ya yi a shekarar 1764 Miladiyya (Gusau, B.M & Gusau, S.M. 2012: 102). Daular Zamfara ta faɗi a hannun Gobirawa a ƙarshen ƙarni na goma sha takwas (Q18).



Wata ƙofa ta mashigin Jihar Zamfara ta Gusau

Bayan tarwatsewar Daular wasu Zamfarawa sun je sun kakkafa wasu sababbin garuruwa da mazaunai daban-daban kamar a Anka da Zurmi da Talatar Mafara da Bakura da Gumi da Kagara da Birnin Zoma da Sauransu
(Dogo, 1982: 68).




Taswirar Wasu garuruwan Zamfara bayan Faɗuwar
Daular Zamfara

Haƙiƙa an yi fafutukar dawowa da mulkin Zamfarawa a matsayi na Daula da Gwamnati tun a zamanin Jihadin Shehu Usmanu Ɗanfodiyo, musamman a wajen ba da

tutoci na cikin gida waɗanda aka ba wasu malamai, musamman Fulani, waɗanda suke Zazzaune a ƙasar Zamfara da wasu garuruwanta sababbi kamar Malam Alu Hamid a Zurmi da Malam Muhammadu Daɗe (1805-1836) a Maru da Malam Muhammadu Namoda a Ƙaurar Namoda da Malam Muhammadu Sambo ɗan Ashafa (1799-1827) a Gusau da Malam Mahmuda a Ƙaurar Namoda da Malam Muhammadu Baciri a Bunguɗu da Malam Gangu a Kannu da Malam Muhammadu Dambo a Gadar Bunguɗu da sauransu.

Haka kuma a 1937 da 1938 Sardauna Sir Abubakar III da Sardauna Alhaji Sir Ahmadu Bello da aka yi yankin Sakkwato Gabas duk sun zauna a wannan shiya ta Zamfara da Katsinar Laka suna gudanar da ayyukan mulki. A daidai wannan lokaci ne kuma aka yi wa wannan yankin ofishin ƙaramin Jami'in Mulki (ADO), mai mazauni a Gusau.

An fara yunƙuri na yaƙin neman Jihar Zamfara tun a shekara ta 1962 (Gusau, B.M & Gusau, S.M. 2012:107). A 1981 aka yi wani yunƙuri na neman Jihar Zamfara. Hakazalika, a shekara ta 1991 Zamfarawa suka ƙara bayyana ra'ayinsu na neman Jihar Zamfara. Mai nema kuwa a ko da yaushe yana tare da samu. Allah cikin ikonsa a ranar Alhamis 1 ga watan Oktoba, 1996. Shugaban Ƙasa Janar Sani Abacha ya tabbatar da ƙirƙiro sabuwar Jihar Zamfara tare da wasu jihohi sababbi. Gwamnatin Tarayya kuma ta ayyana garin Gusau ya zama babban Birnin Jihar Zamfara, kuma aka ba Jihar ƙananan hukumomi har guda goma sha huɗu (14).




Taswirar Jihar Zamfara

A wannan takarda an ƙuduri aniyar bin diddigi gwargwadon lokaci a tsettsefe waɗannan ƙananan batutuwa waɗanda suka ƙunshi ƙwarangwal na wannan tattaunawa kamar haka:

- Wasu hanyoyin raya ilimi da yanayin makarantunsa;
- Wasu hanyoyin ƙarfafa hidimomin rayuwar mutanen Zamfara da tabbatar da jin daɗinsu da saka musu karsashi tare da walwa a ruhinsu.

2.0 Kiyayewa da Raya Ilimi da Makarantunsa

Karatu ko nazari ko neman ilimi abu ne mai sauƙi wanda ƙwaƙwalwa za ta iya fisga da sauri kuma ta sauwara shi ta fuskar koyo da koyarwa, amma kuma abu ne mai rikitarwa tare da tafasa ƙwaƙwalwa ta ɓangaren koyo ba kamar yadda Malamai da iyayen yara za su iya ɗauka ba. Ta haka ne karatu ko nazari ko neman ilimi ya danganci aƙalla abubuwa guda bakwai (7) na yin koyo waɗanda suka haɗa da (i) fahimtar mafitar sauti ko magana (ii) da baƙaƙe (iii) da kalmomi (iv) da ƙwarewa a maganganun hikima na harshe (v) da naƙaltar harshen karatu (vi) da iya rubutu (vii) da kuma insha'i (Zuilkowishi, S.S. & Barnes, A. 2020:1). Ganewa da naƙaltar waɗannan abubuwa guda bakwai (7) su ne sukan zama tsani na fahimtar kowane harshe da mutum yake karatu ko nazari.

Har wa yau kuma a koyarwa ta kowane aji na karatu tana buƙatar a fahimci waɗannan abubuwa da suka ƙunshi dabarun koyarwa da lokaci da littafin karantawa da gwaji da harshe na koyarwa da kuma manhajar koyarwa (Zuilkowiski, S.S. & Barnes, A. 2020:1).

Ya kamata a al'adar karatu ta zamana ta shafi kowa da kowa a Jihar Zamfara kuma ya kasance kowane ɗan Zamfara ya sami wata gudummawa wadda zai dinga badawa ta zama kuma tana rayawa tare da bunƙasa harka ta nema da ba da ilimi a wannan ƙasa ta Jihar Zamfara.

A yanayin karatu da rubutu ana son yara su fara da karatu na labarin kininsu da wasu abubuwa da jininsu ya gada a rayuwarsu. Da haka ne kawai za a sa yaran su dinga tuna baya, su kuma zama masu yi musu tuni da tunasarwa a kan abubuwan da suke koya na gaba da su a rayuwa. Ta haka kuma za su iya kiyaye abubuwa ko su kauce musu ko su dinga aiwatar da su. Haƙiƙa, ta haka za su iya gina rayuwarsu ta gaba, har kuma su iya ƙyaro abubuwa na can nesa da su.



Wasu Ajujuwan Makaranta a Jihar Zamfara a FGG Gusau


Tsayar da nazari ko neman ilimi a yau a Jihar Zamfara wata matsala ce wadda ta dami mutane daban-daban, musamman ma iyaye da Malamai da kuma matasa na waɗannan shakaru na yau. Wannan matsala ce kuma wadda ta fisgi mutane abar kulawa a faɗin wannan Jiha ta zamfara. Ga alama a iya cewa ɓullowar wasu abubuwan more rayuwa na sadarwa tun daga radiyo da talabijin da jaridu da saƙonnin SMS da intanet da Skype da
Email da saƙonnin WhatApp da Facebook da Twitter da makamantan waɗannan abubuwa na wannan zamani sun daɗa taimaka damalmala wannan matsala ta harkar ɗalibtar ilimi a Jihar Zamfara.




Hukumar ZASUBEB Jihar Zamfara, Gusau

Babu shakka, harkar nan ta karatu da tsayar da neman ilimi ita ce take tabbatar da samuwar ingantaccen tsari na ilimi da raya makarantunsa nagari kuma ƙwarara a Jihar Zamfara da duniya baki ɗaya. To hanyar raya ilimi da kulawa da makarantunsa ake iya sunsunar tasirin koyarwar da Malamai suke yi a makarantu, musamman idan za a haɗa ƙarfi da ƙarfi da dukkan sassan bincike na ilimi da cibiyoyin ilimi na manyan Makarantu da Jami'o'in wannan Jiha ta Zamfara da Nijeriya da duniya baki ɗaya.

Al’ada ta neman ilimi tana da wasu hanyoyi waɗanda za a bi ta kansu a raya ta kuma har a gudanar da ita ta zama kammalalliya ko ingantacciya. Ga wasu daga cikinsu:






Jami’ar Tarayya a Jihar Zamfara FAGUS, Gusau




Jamia’ar Jihar Zamfara Talatar Mafara

- Gamsassun Laburare

Bayan kawo littattafai da sauran kayayyakin karatu, ya zama wajibi a kuma keɓe wasu wuraren karatu ko nazari bisa bambancin ajujuwan karatu na ɗalibai da Malamai da Jami’an ilimi da sauransu. Sannan a samar wa kowace makarantar Firamare da ta sakandare waɗannan ɗakunan karatu komi kuwa ƙanƙancinsu. Ba ma sai an yi maganar a samar wa Jami’o’in Jihar Zamfara da manyan makarantu

waɗannan laburare ba. Tsayar da laburare a makarantun Jihar Zamfara zai ba ɗalibai da yara dama kauwame gallar duniya, musamman a matsayinta na yanzu na ‘yar tunga.

- Muɗali’o’in Karatu

Akwai bukatar a dawo da tsarin wuraren karatu da ake kira Reading Rooms a kowace Ƙaramar Hukuma ko gunduma ko wasu garuruwa waɗanda Jami’an ilimi za su zayyai ayyana a Jihar Zamfara. Wannan zai ba mutanen wuraren wata dama wadda za su yi karatu da kansu kuma cikin nutsuwa. iii) Rumfar Sayar da Littattafai na Karantawa

Ya kamata kuma a sami wasu garuruwa fitattu a Jihar Zamfara waɗanda za a ayyana waɗannan wurare na sayar da littattafan manya, sannan a kakkafa musu wurare waɗanda za a raya muhallai na sayar da littattafan karantawa ga jama’a kamar littattafan koyarwa da na ƙagaggun littattafai, na labaru da na wasannin kwaikwayo da sauransu.

- Rumfunan Sayar da Jaridu da Mujallu na Ilimi

Haka kuma ya dace a giggina wasu ɗakuna a wuraren da suka dace a manyan garuruwan Jihar Zamfara waɗanda za a dinga sayar da jaridu da mujallu da sauran takardun ilimi ga yara ‘yan makaranta da sauran ɗaliban ilimi da makaranta da manema labarai da sauran masu sha’awar sanin halin da ƙasarsu take ciki.

- Rumfar Ayyukan Yara

Har wa yau, ya kamata a sami wasu ɗakuna waɗanda za a dinga sayar da wasu ayyuka waɗanda aka yi domin yara. Waɗannan ayyuka na yara sun haɗa da littattafan ilimi na koyarwar yara da na karantawa da littattafan hira na yara watau ƙagaggun labarai na yara, musamman waɗanda aka jejjefa musu hotuna da taswirori da kuma littattafai na insha’i bisa nau’o’insa da littattafai na hotuna kurum da na wasan kwaikwayo tun daga irin na Sauna Jack da makamantansu. Haka kuma a samar da wuraren sayar da ƙananan littattafai na koyar da baƙaƙe da wasulla da sauran ƙa’idojin rubutu da makamantansu.

- Rumfar Ayyukan Masakai

Masakai mutane ne waɗanda suka danganci matsayai daban-daban kamar makafi da mahaukata da guragu bisa nau'o'insu da kurame bisa bambance-bambancensu da marasa hannuwa da dangoginsu da sauran masu matattun zukata waɗanda sukan zauna a cikin wata kama ta shuni da datti da makamantansu.

Ya dace waɗannan mutane a tanada musu wata rumfa ko ɗaki da za dinga ajiye kayayyakinsu na ayyuka waɗanda suka dangance su, kuma waɗanda suka dace da farashi mai rahusa.

Sannan kuma a dinga ƙarfafa musu zama da lazimtar wani lokaci wanda za su dinga yin rubutu da karatu, ta haka ne za a nuna musu yin rubutu don amfanin mutane na gaba masu tasowa a hali irin wanda suka sami kansu.



Kwalejin Mata ta Tarayya, Gusau (FGGC, Gusau)

## 3.0 Ƙarfafa Zukatan Zamfarawa a Kishin Jihar Zamfara

Sana'o'i na saye da sayawa a harkokin kasuwanci a kowace Jiha wani ɓangare ne wanda ya shafi tafiyar da rayuwar al'umma ta yau da gobe cikin sauƙaƙawa da rangwantawa da kawo nesa-kusa. Waɗannan hidimomi su ne suke samar da cikar kamala ta al'adun al'umma da kuma buƙacebuƙacenta. Akwai bukatu da yawa na mutum ɗan'adam waɗanda suka ta'alaƙa da sana'o'in Hausawa na yau da kullum da suka haɗa da:

- Kayayyakin abinci da sauran nau'o'in cimakar Hausawa na ci da na sha;
- Kayayyakin sutura ko tufafi waɗanda suke suturta jikin mutum mai hankali, mai kamala da suka ƙunshi yadudduka da atamfofi da lesuna da shaddoji da sauransu da zannuwa kuma bisa ɗunkuna kala-kala, nau'inau'i tun daga ɗunkin hannu har zuwa ɗunki na na'urar keke;
- Kayayyakin tallafin zaman gida don samarwa bisa bukatu na jin daɗin zaman gida, daɗa kowane iri ne, Gida sabo ne ko kuma tsoho;

- Samar da nama daga dabbobi na gida da na daji da tsuntsaye na gida da na daji da wasu ƙwari da tsutsoci na magani da na abinci, manyansu da ƙanananansu.

- Tanadin kayan miya, musamman mai na girki da tumatur da tattasai da albasa da wasu ganyayyaki na tsirrai da ƙananan itatuwa da dai sauran kayayyaki matallafa aiwatar da miya;

- Tanadin kayayyaki na gine-gine da nau'o'insa kamar sumunti da yashi da katakai da roduna da kwanuka da dirkoki da azaru da sauransu domin a samar da wurin da za a dinga shiga ana hidimomin rayuwa;
- Tanadin sayar da littattafai na addinin Musulunci da na karatun boko da na sauran sassan ilimi na karantawa da na karantarwa da na nazari da na bita da makamantansu;
- Da sauran harkoki na saye da sayarwa da al'ummar Jihar Zamfara suke bukata na tafiyar da kasuwanci.



Wasu sassa na Magizawa Plaza



Wasu sassa na Magizawa Plaza

Haƙiƙa, wajibin mutanen Zamfara ne su samar wa kansu waɗannan kayayyaki da wasunsu domin ta haka ne kasuwanci zai bunƙasa a Jihar, haka kuma ta wannan ne wannan Jiha ta Zamfara za ta sami Alhazai da Attajirai da sauran masu kuɗi waɗanda za su dinga yin harkoki na kasuwanci. Ba a sami wasu mutane kawai daga wajen Jihar ta Zamfara su zama su ne za su tsaya ainun a wajen gudanar da kasuwanci a Jihar ba. Idan Zamfarawa ne suke gudanar da al'amuransu tare da baƙin wasu al'ummu, to za a sami annuri da annashuwa su dinga gudana a Jihar Zamfara har sai ta zama damina mai farar aniya.


Wasan Sharu a Jihar Zamfara

Haka kuma ba sai an nuna ko an faɗa ba, ya dace Zamfarawa na Jihar Zamfara, su tsaya tsayin daka, su raya wannan Jiha tasu, su nuna mata soyayya ta zucci da ta zahiri, su dinga tsayawa a ƙasarsu ta Zamfara suna yin sayayyarsu, ba sai sun tafi wasu birane ko garuruwa ko har sai sun yi wata ƙaura ba.

Alalmisali, idan har 'yan kasuwar Zamfara suna zuwa Kano ko Sakkwato ko Abba ko Jega ko wasu ƙasashen waje su sayo kayayyaki don su sayar a Jihar ta Zamfara, to ashe ya kamata su mutanen ƙasar Zamfara su tsaya a gida su dinga aiwatar da duk wata sayayyarsu. Babu buƙata a fita wajen Zamfara domin wasu 'yan kasuwa, majiɓinta kasuwanci sun ɗauke musu wannan nauyi.



Ƙofar Shiga Wata Kasuwar Gusau daga 1952



Wani Ɓangare na Kasuwar Gusau wadda aka gina a 1952



Wani Sashe na Kasuwar Anka



'Yanlemo da Mangwaro a Kasuwar Anka



Wani Yanki na Kasuwar Talatar Mafara Wadda ta Shahara da ci a Ranar Kowace Talala

Idan aka dubi Jihar Zamfara da idon rahama, za a tabbatar da wajibin kowane mutumin Zamfara ne ya sa hannunsa a ginuwarta ta kowane gefe mutum yake hidimominsa. Alalmisali ta ɓangaren ilimi ne ko ta gefen kasuwanci ko ta sashen samar da bukatun gida ne ko ta samar da abubuwan walwalar jama'a ko ta kulawa da tsabtace ƙasa ko ta inganta yanayin tsara samar da kirkizar iyali da sauran Jama'ar ƙasa ko ta kiyaye lafiyar matafiya a duka hanyoyi na ciki da na wajen Jihar Zamfara ko ta samar da hanyoyin tarbiyya da girmama jama'a, manya da yara, maza da mata ko ta sauran auran hidimomi da ma'amalolin rayuwa ta yau da kullum a faɗin Jihar Zamfara da kewayenta.



Ƙofar Shiga Kwalejin Ilimi ta Maru, Jihar Zamfara

Wasu Sassa na Kwalejin Ilimi ta Maru, Jihar Zamfara

Daga nan kuma ya dace a daɗa giggina rumfuna na kanikanci tun ma ba keɓaɓɓun shaguna kuma ginannu ba waɗanda za a yi domin harka ta kula da lafiyar motoci na Jihar Zamfara.

Maganar tsaro a Jihar Zamfara muhimmiya ce kuma ta musamman, tun ma ba yadda ta addabi kowa da kowa a Nijeriya ba. Wajibin Gwamnati da mutanen Jihar Zamfara su samar da dabarun aiwatar da tsaro da zuciya ɗaya tare da kyautace niyya domin Allah. Musamman dabarun na tsaro a Jihar Zamfara a yi su su dinga tafiya kafaɗa da kafaɗa da na zamanin yanzu, sannan kuma a nace naciya a wajen yin addu'o'i daga kowa da kowa, musamman addu'o'i na Malaman addinin Musulunci da na yara da na mata. Haka kuma a dinga neman shawarwari a tsakanin mutanen Zamfara da kuma ma na ƙetarenta.


Wasu Zamfarawa a Yanayi na Tsoro

Abin lura ne ga mutanen Zamfara su kula da kiwon lafiyarsu tun daga tsabtace jikinsu da tufafinsu da muhallinsu da sauran abubuwan bukatunsu. Wajibi ne Zamfarawa da kansu su damu da lafiyarsu, musamman su damu da neman magunguna na cututtukan da suke damun su tun daga magani na al'adar Hausawa da na zamani a asibitoci da

neman likitoci da sauran jami'an lafiya. Wannan abu ne da Hausawa suka saba yi ba sai sun jira an yi musu ba domin gyarta kayanka ne wanda bai zama sauke mu raba na.

Amma duk da haka yana daga cikin ayyukan Gwamnatin Jihar Zamfara ta kula da sha'anin lafiyar mutanenta tare da kawo magunguna waɗanda suka dace da ma'aikatan ayyukan asibitoci da wuraren shan magani kamar asibitoci, sannan ta samar da likitoci da nurse-nurse da unguzomomi da sauran duka ma'aikatan jinya waɗanda za a tuttura su a kowane lungu na Jihar Zamfara. Haka kuma akwai buƙatar masu arziki watau attajiran Jihar Zamfara su dinga tallafa wa Gwamnati ta fuskar harkar lafiya a Jihar Zamfara domin a samu a iya rarakar cututtuka a tsakanin mutanen Zamfara a Jihar Zamfara.



Wasu Zamfarawa Suna daɗa Motsa Jikinsu a Ziyarsu ta Wata Gona

Wani abin lura a nan shi ne ya fi zama a'ala mutanen Zamfara su dinga zaɓen mutanen Zamfara kammalallu da dattawa musamman ma waɗanda suka cika aƙalla daga shekaru arba'in (40) a duniya masu imani da Zamfara, su dinga ɗora su a kowane ɓangare na shugabanci ko jagoranci. Wannan zai sanya Jihar Zamfara da Zamfarawa su dinga amsa nagartattun sunayensu kuma har su zama masu ainihin kwaikwayo da biyar sawun magabatanta na farko tun ma ba irin su Shehu Usmanu Ɗanfodiyo da Sheikh Abdullahi na Gwandu da Sheikh Muhammadu Bello Sarkin Musulmi da Sheikh Muhammadu Sambo Ɗan'ashafa da Sheikh Muhammadu Namoda da Sheikh Abu Hamid waɗanda suka yi jihadi a sashen Zamfara da Sakkwato da Arewa da faɗin Nijeriya.

## 4.0 Kammalawa

Wannan takarda ta yi bayani ne a kan Jihar Zamfara, musamman dangane da raya ta da ƙarfafa ta ta fuskar neman ilimi da makarantunsa na koyon ilimi da kuma wasu hidimomi na rayuwar mutanenta waɗanda suke nuna kishisunsu a zuciyoyinsu.

A wannan rubutu, an nuna karatu wata hanya ce wadda take ƙarfafawa tare da tabbatar da inganci da kuma aminci na ilimi a zango na gaba. A wata hikimar magana ta

Hausawa cewa ta yi, ‘yi ajiya a baya domin ka tsince ta a gaba’. Ta haka ne kuma aka nuna, ‘fahimta ta rayuwa da hikima ta fuskar rayuwa, duka ba za a same su ba, sai ana da faffaɗan karatu da yin lazume-lazumen nazari tare da kutsa kai cikin tarihi. Daga nan ne kuma Malami mai amfanar da ɗalibai a kowane zango, zai zama shi ne wanda yake da zuzzurfan karatu, wanda kuma ya yi karance-karance har ya zama a kowane fage kaifi ne, watau ya karanta can kuma ya karanta nan.

Domin haka, akwai bukatar a koyarwa, dukkan waɗanda suka jiɓinci wannan hidima ta koyarwa su haɗa ƙarfi, su jajirce, su dinga gudanar da aikinsu bisa amana da kyautayi. Haƙiƙa, tun daga masu shiryawa tare da tsara dokoki na koyarwa, musamman Malamai masu koyarwa da iyayen yara da ƙungiyoyinsu da sauran mutanen Zamfara su sa hannunsu a wajen samar da ilimi da giggina makarantunsa a wannan yanki na Jihar Zamfara.

Haka kuma lokaci ya yi a wannan marra da aƙalla a sami daidaito a wajen nauyin ilimi a tsakanin wanda ya yi karatu a makarantu masu zaman kansu da kuma a makarantu na Hukuma ko na Gwamnati. Wannan zai sanya a dinga bin dokokin koyarwa gadan-gadan a kowane ɓangare na waɗannan makarantu. Wannan kuma zai ba da dama ga kowane sashe na mutanen ƙasa da kuma na Gwamnati su dinga kiyayewa tare da tsare haƙƙoƙin ilimi daidai iyawa ba tare da nuna gajiyawa ko wuce gona da iri ba.


Akwai bukatar Zamfara su ƙara amincewa da Jiharsu ta Zamfara, kuma su fahimci an yi ta ne dominsu kuma ya kamata su yi matsi wajen gudanar da harkokinta da tafiyar da al’amuranta na rayuwa, musamman yadda Allah ya hore wa mutanen Zamfara baiwoyi na tafiyar da al’amuran rayuwa iri-iri.

Tabbas kuma ya kasance ‘yan Zamfara ne za su fara dagewa a kan yi wa Jihar Zamfara abubuwa waɗanda za su bunƙasa ta ba tare da nuna wani son kai ko ainihin son mutum ya cim ma wasu burace-buracensa ba.

Sannan kuma matasa a Jihar Zamfara, manyansu da ƙananansu, kuma ba tare da nuna bambancin inda suka fito ba, su dinga dogara da kansu a muhallan aiwatar da bukatansu, ba sai sun tsaya suna kallon Gwamnati ko wata hukuma su yi musu ba, musamman idan abun bai tsananta ba, domin ba wajibi ne mutum ya ɗauki kayan da bai iya ɗauka ba, musamman kuma Hausawa na cewa ‘kashin baƙi sai taro’. Dubi wannan bishiya ta matasa na Hausawa da kuma a Jihar Zamfara:

Bishiyar Matasa

Su kuma mata masu juna biyu ya kamata su ƙara kula da kansu, musamman lafiyarsu da ta jariran da suke ɗauke da su tun samun cikinsu, haƙiƙa wannan kulawa ita ce ta ƙashin kansu sai kuwa majiɓinta al'amuransu. Mai ciki za ta kula da cimakar gargjaiya ta gado da magunguna aƙalla na zamani da na gargjaiyar Hausawa da saka tufafin da suka dace da makwanci wanda ya dace da sauran abubuwan rayuwa da suka dace da al'adunsu. Ta haka ne mace mai ciki za ta sami sauka lafiya kuma ta sami sauƙi cikin sauƙaƙawa.



Wata Matar Zamfara mai Juna Biyu

Ya kuma dace ga mutanen Jihar Zamfara su fahimci, Allah ne ya halicci komi ko kuma kowane irin abu, Allah ne ya halicce shi a kan tsari. Tsarin nan ya ƙunshi na wurin zamansa ko al'adunsa na rayuwa ko rarrabuwar ayyukansa bisa sashe a kan sashensu ko ma'amalolinsa ko dukkan abubuwan da suka danganci mutum. Allah ya ce:

﴿إنا كل شيء خلقنه بقدر # سورة القمر ألية49 ﴾

Ashe ke nan wajibin Zamfarawa ne su ɗaukaki Jiharsu ta Zamfara kuma su ƙarfafa ta ,sannan su tallafa wa junansu bisa sashensu ,su taimaki wanda ya kasa da duk abin da ya sauwaƙe musu .Wannan shi ne abin da Manzon Rahama ya ambata a cikin Hadisi na 32 Ruwayar Imamu Malik a Al-Muwaɗɗa inda yake cewa ,)ال ضرر والضرار( : watau a' Musulunci babu cuta ba kuma cutarwa .'A wani Hadisi na ,32 Manzon Allah , sallallahu Alaihi Wa Sallama ,yana nuna' ,Musulmi ɗan'uwan Musulmi ne watau ya taimake shi kuma ka da ya yi masa duka wani abu na cutarwa( المسلم أخ المسم) :Ƙaura ,S.A. 2017 .Tarjamar Al-Arba'in Nawawiyya .Zaria :Ahlu-Lah, for Printing and Distribution .)

Haka kuma ina sake nanata, alhakin 'yan Jihar Zamfara ne su tsaya tsayin daka su yi wa Jiharsu duka muhimman hidomin da take buƙata, ba su je su dinga gyara waɗansu wurare ko jihohi ba. Lalurarmu a cikin Jihar Zamfara mu taimaka, mu sa wa Jiharmu annuri, mu dinga biya wa kanmu buƙatunmu. Kada mu rungume hannuwanmu sai

Gwamnati ta 20 ta yi mana abubuwa domin Gwamnati ba za ta iya yaye buƙatun Jiharta ita kaɗai ba, sai ‘yan Jihar sun yi mata ɗauki a wasu ayyuka.

Dubi Annabin Allah, Manzon Rahama, Sallallahu Alaihi Wa Sallama daga Hadisin Abuhuraira inda yake cewa, ‘Duk wanda ya yaye wa wani mumini wani baƙin ciki daga cikin baƙin cikin duniya, Allah zai yaye masa baƙin ciki daga cikin baƙincin lahira, duk wanda ya taimaka wa maras shi, Allah zai taimaka masa a duniya da lahira, duk wanda ya rufa asirin Musulmi, Allah zai rufa masa asiri duniya da lahira, Allah mai taimakon bawa ne matuƙar yana taimakon ɗan’uwansa. Duk mutumin da ya bi hanyar neman ilimi, Allah zai sauwaƙe masa hanyar zuwa Aljanna, mutane ba su taɓa haɗuwa a ɗaya daga cikin ɗakunan Allah suna karanta littafin Allah da nazartarsa, rahama kuma sai ta lulluɓe su, Mala’iku kuma za su yi haba-haba da su, Allah kuma ya ambace su cikin makusantansa, duk mutumin da aikinsa ya yi sanadiyyar kasancewarsa a baya, to nasabarsa ko dangantakarsa ba za ta mayar da shi a gaba ba. Muslim ya ruwaito wannan lafazi (Ƙaura, S.A. 2017. Tarjamar Al-Arba’in-Nawawiyya: sh. 106-107).

Manazarta

Alƙur’ani, mai tsarki.

Abdullahi, S.U. 1984. On the Search for a Viable Political Culture. Reflected on the Political Thought of Sheikh Abdullahi Ɗanfodiyo. Kaduna: NNN Commercial Printing Department.

Abubakar, S. 1982. Birnin Shehu: The City of Shehu: A Social and Economic History. Kundin Digiri na Uku. Zaria: Department of History, Ahmadu Bello University.

Adamu, M. 1978. The Hausa Factor in West African History. Zaria: Ahmadu Bello University Press & Ibadan: Oxford University Press.

Adamu, Y.M. 2020. Zamfara: Poverty, Ignorance, Poor, Halth and Trial of a People. Takardar da ya Gabatar a Babban Taro na Huɗu na Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci. Sakkwato: Jami’ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Ajayi, J.F.A. & Crowder, M. 1971. History of West Africa. Vol. I. London: Longman Group Limited.

Ajayi, J.F.A. & Espres, L. 1965/1977. A Thousand Years of West African History. Ibadan: Nelson & Univesity Press.

Alƙali, M.B. 1969. A Hausa Community in Crisis: Kabi in the Nineteenth Century. Kundin Digiri na Biyu. Zaria: Sashen Tarihi, Jami’ar Ahmadu Bello.

Anka, Y.M.S. 1991. A Case for Creation of Zamfara State. Gusau: Idris Printing Company Limited.

Augi, A.R. 1984. The Gobir Factor in the Social and Political History of the Rima Basin C. 1650-1808. Kundin Digiri na Uku. Zaria: Sashen Tarihi, Jami’ar Ahmadu Bello.

Baƙo, A. 2020. The Significance of Birnin Zamfara Era in the History of Zamfara Kingdom. Takardar da ya gabatar a Babban Taron Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci. Sakkwato: Usmanu Ɗanfodiyo University.

Bello, M. 1964. Infaƙul Maisuri (Larabci). Sakkwato: Sardaunan Sakkwato Alhaji Sir Amadu Bello, Firimiyan Jihar Arewa ya buga.

Chafe, K.S. 2016. Zamfara State; its History, Challenges and Prospects in the Northern Federation. Public Lecture Presented at the 20th Anniversary of the Creation of Zamfara State. Gusau: Ɗa'a Press Limited.

Chafe, K.S. 2020. Zamfara in Historical Perspective: A Synopsis of the Social and Political Transformations in Zamfara Land Since the Sixteenth Centuary C.E. Takardar da ya Gabatar a Babban Taron Tsangayar Fasaha da Addinin Musulunci. Sakkwato: Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

CNHN. 2006. Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria: Ahmadu Bello University Press. Limited.

Committee on the Movement for the Creation of Zamfara; 1996. A Case for the Creation of Zamfara State Out of the Present Sokoto State. Kaduna: Street Typographic Press.

Ɗangusau, A.M. 1998. Who is who in Zamfara State. Kaduna: Mega Press Nigeria Limited.

Dogo, A.M. 1973. Political History of Zamfara from C.A. 1764 to the Jihad. Kundin Digirin Farko. Zaria: Sashen Tarihi, Jami'ar Ahmadu Bello.

Dogo, A.M. 1982. Gudanar da Mulkin Daular Zamfara a Cikin Zaruma: A Cultural Magazine of Sokoto State. February, 1982. Sokoto: The Council for Arts and Culture.

Gusau, B.M. & Gusau, S.M. 1979&1984. Gusau ta Malam Sambo. Zaria: Ganuwa Publishers.

Gusau, B.M. & Gusau, S.M. 2012. Gusau ta Malam Sambo (Sabon Tsari). Kano: Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S.M. 1988. Waƙoƙin Makaɗan Fada: Sigoginsu da YanayeYanayensu, Vol. II. Kundin Digiri na Uku. Kano: Sashen Koyar da Harsunan Nijeirya, Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. & 1987. Taƙaitaccen Waiwaye a kan Kafuwar Wasu Garuruwan Ƙasar Hausa. Takarda Wadda ya Gabatar. Sokoto: Ma'aikatar Ilimi, Sashin Kimiyya da Tarbiyyar Malamai.

Gusau, S.M. & Funtua, A.I. 2010. Al'adu da Ɗabi'un Hausawa da Fulani. Kaduna: El-Abbas Printers and Media Concept.

Gusau, S.M. 1994. Ƙasar Zamfara: Tsokaci a kan Neman Jiha. Takardar da ya Gabatar Domin Neman Jihar Zamfara. Gusau: Makarantar Sakandare ta Gwamnati.

Gusau, S.M. 2015. Fulanin Zamfara-Katsina Laka da Tasirinsu a Daular Sakkwato. Kano: Century Research and Publition Limited.

Ƙaura, S.A. 2017. Tarjamar Al-Arba'in Nawawiyya. Zaria: Ahlul-Lah for Printing and Distributions. Pinted by Cairo: Daral-Hahad Li l-Tiba'ah, Dar al-Salam.

Nadama, G. 1979. Urbanization in the Sokoto Caliphate: A Case Study of Gusau and Ƙauran Namoda a Cikin The Sokoto Seminer Papers. Y.B. Usman (ed). Sokoto: History and Culture Bureau.

Umar, M.B. 1980. Al'adun Hausawa a Ƙasar Hausa. Zaria: Hausa Publication Centre.

Zamfara State of Nigeria. 2011-2013. State Education Sector Opertioinal Plan (SESOP). Kaduna: Kaina Press.

Zamfara State of Nigeria. 2012. Report of the Zamfara State Primary Education Assessment Committee. *Vol*. I Main Report. Abuja: Tulip Press.

Zamfara State of Nigria. 2010. State Education Sector Strategic Plan (SESP). Kaduna: Kaina Press.

Zamfara State. Creation Committee. 1981. *Requiest for the Creation of Zamfara State*. Kaduna: One Nigeria Press.

Zaruma: A Cultural Magazine of Sokoto State. 1978. Sidi Umaru Printing Press.

Zaruma: A Cultural Magazine of Sokoto State. 1982. Sakkwato: Sidi Umaru Printing Press.